JAGORAR

HAQQOQIN DAN ADAM DA GARKUWAR DOKA

Na

# AYYUKAN KULA DA LAFIYAR MATASA DA BAYANAI AHIP KANO – NIJERIYA

WACCE TA TACE

**Mairo V. Bello**

Darakta/Shugabar kula da shirye-shirye AHIP

2000

JAGORAR HAQQOQIN DAN ADAM DA GARKUWAR DOKA

**WALLAFAWA**

# AHIP

**BABBAN OFISHI**

**CIBIYAR AHIP,**

**PLOT 9, TARAUNI MARKET ROAD,**

**P.O. BOX 12846, KANO – NIGERIA**

**TEL: 062-667286 FAX: (234) 064-663193,**

**Email: ahip@samdar.com  ahip@gclonline.com achip@gclonline.net**

**RASSA**

**JIHOHIN JIGAWA DA BAUCHI**

**<u>HAQQIN DAN ADAM</u>**

**MANUFOFI**

*Bayan karanta wannan littafi a qarshe makaranta za su :*

- *Yin Kyakkyawar fahimta akan haqqoqin xan adam*
- *San abubuwan da suka kare haqqoqin xan adam*
- *San dalilan da su ka sa za su tsaya domin qwato haqqoqinsu*
- *Sanin wasu daga cikin take haqqoqin xan adam.*

## <u>GABATARWA</u>

Batun haqqoqin xan adam ya samo asali ne tun kafin kafuwar majalisar xinkin duniya. Sai dai kuma sai da aka kafa qungiyar ne, batun ya kafu da kyau kuma ya karvu a duniya. Tarihin haqqoqin xan adam abu ne mai xaukar hankali, ya samu ne daga dukkan muhimman al'amura da suka auku a duniya, sannan kuma gwagwarmayar ta xore domin tabbatar da samun 'yanci da zama xaya a ko'ina.

Al'ummar duniya ta havaka, kuma ta samu gagarumin canji a cikin qarni na ashirin, wanda hakan ba ta samu ba har sai bayan da aka kai ruwa rana, game da yaqin duniya na biyu wanda ya jawo waxanda suka yi nasara suka samar da wani tsarin, da farko saboda su yi maganin wasu abubuwan da su ka faru a lokacin yaqi, sannan kuma a samo hanyoyin da za a bi domin a hana faruwar hakan a gaba. Waxannan ba kowa ba ne sai Majalisar xinkin duniya.

Har yanzu ana sane da shirye-shiryen da ake da su a qasa, kamar yadda aka so a ce an samar da wasu abubuwa waxanda za su taimaka wajen ganin cewa an tabbatar da haqqin xan adam. Kafuwar 'yancin xan adam ce ta samar da ginshiqin da aka kafa walwalar al'umma a kai, wanda wannan ne ya samar da ci gaba

An tabbatar da gagarumin aikin da ke gaban qungiyar, wanda abu ne da ya ke a fili a lokacin, da kuma zuwa yanzu. Saboda haka qoqarin fayyace yarjejeniya daban-daban na duniya a game da haqqoqin xan adam su ka ci gaba da zama muhimmai ga kowa da kowa. Kafuwar 'yancin xan adam

ce ta samar da ginshiqin da aka kafa walwalar al'umma a kai, wanda wannan ne ya samar da batutuwa na kare haqqin xan adam, sun samar da ginshiqi wanda akan sa ne fasalin tsarin siyasar yancin xan' adam ta dogara; Sannan 'yancin xan' adam ya haifar da buri da kuma damar ci gaban tattalin arziki da zamantakewa da kuma samar da ginshiqin kwakkwaran zama lafiya.

Mutane qalilan ne suka yaba da nisan da shirin ya yi tun shekarar 1945, har ila yau, babban qudirin dai ya ci gaba da zama yarjejeniyar duniya ta kare haqqoqin xan adam da aka zayyana a sama, kuma aka soma qullata a 1948. Yarjejeniyar ta tsara muhimman haqqoqi da ake so kowane mutum a duniya ko da kuwa shi wace qabila ce, ko launinsa, ko jinsinsa, ko yare, ko addini, ko siyasa, ko ra'ayinsa, ko usulinsa, ko dukiyarsa, shekaru da duk wani matsayi na shi.

A babban taron duniya da aka yi akan haqqoqin xan adam a garin Teheran, da ke qasar Iran, a 1968, domin duba nasarorin da aka samu daga lokacin da aka qulla yarjejeniyar ta duniya akan haqqoqin xan adam, da kuma tsara wata manufa da za a sanya a gaba, taron ya yanke shawarar yin qira ga dukkan qasashe da su tabbatar an "bi dukkan hanyoyin ilmantarwa' ta sanarwa matasa damar girma cikin mutunta martabar xan adam da kuma haqqoqi iri guda.

Su na ganin cewa maqasudin wannan ilimi shine samar da cikakkun bayanai da damar yin zantuttuka, suka kuma kwaxaita yin amfani da shi da duk wasu abubuwan da ya qunsa,domin su taimaka wajen qarfafa matsalolin da ake da su na canja duniya, sannan kuma su shirya matasa zuwa ga rayuwa ta zamani.

**MA'ANA**

Bil'adam na nufin kowanne irin mutum.  Haqqi kuma na nufin. Haqqin da ya dace, na zahiri, qwaqqwara, dai dai wa dai da, sannan kuma ya yi dai dai da doka. Yana kuma nufin adanawa (a nan yana nufin adana duk wani abin da yake da muhimmanci kuma mai ma'ana).

Saboda haka haqqoqin xan adam dokoki ne da aka tattara su, waxanda ke yin gyara, wasu lokutan kuma su adana rayuwar mu da maganganun mu, mu zamo yan adam ma su qima da daraja a doron qasa.

Haqqoqinmu na 'yan adam da kuma 'yancin da mu ke da shi ne ke bamu damar bunqasa har muka cika martabar mu ta yan adam, domin mu wadatar da zukatanmu. Hakan ya samo asali ne a sanadiyyar burin da xan adam ke da shi na son gina kan shi da rayuwar shi saboda ya samu xaukaka ta yadda sauran yan adam za su samu mutunci da kuma kariya.

Hana xan adam Haqqoqinsa da kuma Muhimman ‘yancin sa, ba wai ya shafi shi Mutum shi kaxai ba ne, har ila yau hakan na haifar da yanayi na rashin kwanciyar hankali ta fuskar zamantakewa da siyasa, da kuma shuka tashin hankali da rikici a ciki da kuma tsakanin al’umomi da qasashe. Kamar yadda jimla ta farko ta yarjejeniyar kare haqqoqin xan adam ta duniya ke cewa mutunta haqqoqin xan adam da kuma martabar sa “shine tushen yanci, da adalci da kuma zama lafiya a duniya.

Qulla yarjejeniyar da aka yi ta kare haqqoqin xan adam gagarumar nasara ce ga ci gaban rayuwa. Tarihin haqqoqin xan adam na bayani filla-filla akan qoqarin da aka yi na fayyace martaba da darajar xan adam da kuma muhimman haqqoqin sa, shi dai wannan qoqari ya ci gaba har zuwa yau. Qoqarin qwato haqqi na yanci da na siyasa, tare da gangamin hana bauta (bayi), faxan qwato tattalin arziki da na zamantakewa, su suka yi sanadiyyar taron qulla yarjejeniyar kare haqqoqin xan’adam da kuma wasu irin waxannan tarurruka guda biyu da suka biyo baya, da kuma dukkan tarurrukan da yarjeniyoyin da suka biyo bayan wannan, aka yi tanadin dokoki domin aiki da su.

Ana dannewa mata haqqin su, a cin mutuncin haqqoqin na su, har ma a yi watsi da su ,ko ma a qi amincewa da haqqoqin gaba xaya saboda kawai maza ne su ka zauna su ka tsara hakan a wurare daban daban. Misali, haqqin mallakar dukiya, ba yana nufin haqqi ne na mallakar sauran jama’a a matsayin dukiya ba(bayi da mata), mazan da ke da matsakaicin matsayi sannan suke da  isasshen abinci, da makwanci mai kyau, da isasshen kuxi da nagartaccen ilmi, na mayar da hankali ne ga haqqoqin samun ilmi, abinci da kuma kyautata rayuwarsu.

Dukkan abubuwan da ke cikin haqqoqin xan’adam sun qunshi buqatu da damuwar waxanda suka tsara su. Babbar fahimtar mene ne haqqoqin xan adam a kowanne lokaci ya dogara ne akan qarfin da jama’ar da ke da hannu cikin wannan qoqari ke da shi.

Ana hana mutane haqqoqinsu a wasu lokutan saboda addini, al’adu da kuma dabi’u. misali a wasu al’umomin mutanen da ke da launin fata baqa ana qasqantar da su, wanda har ta kai ba a basu ‘yanci’ iri guda da masu farar fata.

Al’umma na da tunanin cewa mata qasqantattu ne masu rauni. Saboda haka sai dai  kawai su tsaya a gida su yi girki, su bar al’amuran qasa ga maza.

Har ila yau, akwai maganar ‘Yancin tsare mutum da kuma yin shari’a cikin adalci tare da  zaman sauraron jama’a  a kotun musamman mai zaman kanta. Sannan kuma a samu ‘yancin zirga-zirga da shiga qungiya da zaven addini da kuma samun sirri a tsakanin ka da iyalan ka da wurin aikin ka.

Dukkan waxannan haqqoqi ne na xan adam da tsarin shari'a ta Nijeriya ta tanadarwa xan qasa su saboda tsarin mulkin qasar ya yi tanadin hakan. Akwai kuma sauran dokokin da ba a wajabta su ba.

a) 'Yancin yin aiki da kuma karvar wadataccen lada.
b) Samun nagartacciyar rayuwa
c) Samun tsaro na zamantakewa da kuma lokacin nishaxi
d) Samun dama iri guda ta xaukar aiki da kuma haqqoqin samun abinci.
e) Ayyukan kula da lafiya da kuma ilimi.

Dangane da haka haqqoqin xan adam sun haxa da: na siyasa, na cika xan qasa, na tattalin arziki, na zamantakewa, na al'adu, na sana'a, na jima'i da vangaren qaruwa da dai sauransu. Dukkan waxannan Haqqoqi an amince da su a yarjeniyoyi na duniya. Saboda haka in ana so haqqoqin xan adam su ci gaba da yin tasiri sosai a duniya a rubuce da kuma a aikace, to haqqi ne da ya rataya a wuyan kowa ya yi qalubale da kuma gwagwarmayar qarin haske domin baiwa kowa damar aiki da amfana da haqqoqin.

**WASU DAGA CIKIN TARURRUKAN QULLA YARJEJENIYAR KARE HAQQOQIN XAN ADAM.**

1. Kundin dokoki na qasashen duniya akan haqqoqin xan'adam da majalisar xinkin duniya ta tsara a 1947 sun qunshi.
    a) Yarjejeniyar duniya akan haqqoqin xan'adam ta 1948 wanda babban taron majalisar xinkin duniya na ranar 10, shekarar 1948 ya amince da shi. Ita wannan yarjejeniya ta qarfafa yancin xan adam a matsayin wani wani ma'auni na ci gaban al'umma da qasashe
    b) Taron qasashen duniya akan haqqoqin tattalin arziki,da zamantakewa da kuma al'adu na shekarar 1976.
    c) Zuwa shekarar 1980 qasashe 95 ne suka amince da taron, wanda yake tabbatar da cewa dukkan jama'a suna da haqqoqi na 'yancin kai' da cimma burin kai, kuma akwai yancin yin amfani da wannan haqqi ba tare da nuna bambancin al'uma, ko launi, ko jinsi, ko harshe, ko addini ko siyasa, ko ra'ayi, ko qasa ko usuli na zamantakewa, ko dukiya, ko haihuwa ko dai wani matsayi ba.
2. Taron Qasashen duniya akan haqqoqi da suka shafi 'yanci da kuma na siyasa 1976 – 92 ya bayyana cewa kowa yana da haqqi na rayuwa, na ya zava ko a zave shi, yancin tunani, haqqin hana azabtarwa ko ladabtar da mutum, 'yancin zirga-zirga (walwala) da kuma kasancewar kowa xaya ne a gaban doka.

3. Yarjejeniyar Afirka akan haqqin Xan'adam da kuma jama'a na shekarar 1981. Wannan yarjejeniya ce da aka qulla domin xaukakawa da kuma kare haqqoqin mutane da qasashen da ke cikin qungiyar haxa kan Afirka (OAU).

4 Yarjejeniyar duniya akan haqqoqin Xan'adam (Babi na 2) na cewa kowanne mutum yana da dukkan waxannan haqqoqi da yanci da aka zayyana a cikin wannan yarjejeniya ba tare da nuna wani bambanci kowanne iri ba, kamar al'uma, ko launi, ko ra'ayi, ko usuli na qasa ko zamantakewa, ko dukiya, ko haihuwa ko dai wani matsayi ba.

## TAKE HAQQOQIN MATA

- Ba wa 'ya'ya maza fifiko.
- Wasu al'ummar na tsarawa yara maza da mata irin rawar da kowanne zai taka, da matsayi daban-daban da ake sa ran nan gaba za su kai, da kuma bambanta yanayin shekaru na yin aure.
- Tsarin a dake ka a hana ka kuka, ma'ana (maza ne kawai za su fi samun biyan buqata wajen jima'i).
- Tsananta zancen budurci ga yara mata kawai banda yara maza
- Yi wa mata kaciya da sauran al'adu da ake yi wa mata
- Taqaita shugabanci ga yara maza kaxai
- Yara mata kuma su yi girki, talla, ayyuka na cikin gida da kuma kula da yara.
- Mata kan sadaukar da rayuwar su, musamman wajen haihuwa, amma duk da haka ba a basu damar bada shawara akan wasu al'amura.
- Maza ne ke da 'yancin riqe yara idan aure ya mutu.
- Mata ba su da ikon gado
- Bambanci a wajen gudanar da ayyukan gida, a yau akwai mata da dama da suka yi fice wajen riqe muqamai masu muhimmanci, amma duk da haka sai ta yi ayyukan gida.

## HAQQOQIN MATA VANGAREN QARUWA A NIJERIYA

Tsarin shariar Nijeriya ta kuma tavo haqqoqi na vangaren qaruwa, domin kuwa dokokin da aka tsara su bayan an samu tsarin dokoki na turanci, suna tafiya ne kafaxa-da-kafaxa da dokoki na gargajiya.

Ana kuma ganin dokokin gargajiya kamar yadda muka sani a tsarin zamantakewa na gargajiya, tsari ne da aka samo shi sakamakon mulkin mallaka, da aka tanade shi a matsayin makami na gudanar da tsarin mulki 'Lord Lugard, kuma babu wani tsari da ya bi ta qarqashin wannan tsari, da ba a yi masa illa daga anihin tsarin sa ko fasalinsa ba. Wannan ke nuna cewa hanyoyin da za'a bi za

su kasance nesa-nesa da dokar gargajiya. Aikin da ke gaban dukkan masu qoqarin kyautata Nijeriya shine samun matsaya guda da tsari na bai xaya kuma mai ci gaba da aka tattaro shi daga qasaitaccen tarihin mu na abinda mu ka koya.

Nijeriya ta amince da mafiya muhimmancin yarjeniyoyin na qasashen duniya da suka zayyana haqqoqin da mata suke da su na vangaren qaruwa. Saboda haka Nijeriya ma za ta yi amfani da waxannan haqqoqi wajen kyautata vangaren qaruwa da lafiya.

Bayan waxannan, akwai muhimman dokokin da ke qunshe cikin kundin tsarin mulkin mu kamar haka;

a) Kundin Tsarin mulkin Nijeriya na (1979) da ya kare mata daga wani nau'I na wariya saboda jinsinsu sannan kuma ya ba su dukkan haqqoqinsu na mtsayin su na 'yan qasa ta fuskar walwala da siyasa.

b) Yarjejeniyar qasashen Afirka akan haqqoqin xan'adam da na jama'a (an amincewa da ita da kuma yin aiki da ita) (*act cap 10*) dokokin qungiyar (1990), sun qara duba haqqoqi da aikace aikace na tattalin arziki da zamantakewa da al'adu.

Abubuwan da aka lissafa a sama sune irin kariyar da matan Nijeriya ke da Haqqi a basu. Waxannan haqqoqi ya kamata su fayyace dukkan abubuwan da ke qunshe cikin batun ya jivanci haqqoqin da mata suke da shi na vangaren qaruwa, ko dai daga tsarin ingilishi ko na Nijeriya.

Sai dai abin lura anan shine waxannan dokoki sau da yawa suna nan a rubuce ne kawai a liffattafai. Sau da yawa jama'a ba sa aiki da su. Babu dalili na ci gaba da cirewa waxannan haqqoki ko kuma a ce wai saboda sauyi na shugabancin Nijeriya shi ne ya sanya ake watsi da batun, ya kamata Nijeriya ta yi koyi tare da rungumar waxancan yarjeniyoyi domin a samu sauyi na cigaba.

## CIN MUTUNCIN YARA

Yana da muhimmanci a ce babban abin da kowace qasa ta sa a gaba a yanzu shi ne wadata yara domin su sami managarciyar rayuwa a gaba ta yadda al'umma za ta ci gaba da bunqasa. Wannan mai yiwuwa, shi ya sanya tun farkon qarnin da ya gabata , qasashen duniya ke ta xaukar matakai na jaddada, da kuma kare haqqoqi da buqatun yara. Taro na farko da aka fara gudanarwa a shekarar 1909 a fadar Amurka (white house) akan yara, ya amince da cewa yara wani rukuni ne da ke cikin al'uma, wanda ya ke da haqqoqin da ke buqatar kariya. Baki xayan yankin da ya yi magana akan yara na (1930) taron fadar Amurka da kuma yarjejeniyar da babban taron majalisar xinkin duniya ta qulla a 1959 akan yara, ya amince akan dole ne magidanta su ba wa yara cikakkiyar kula, ma'ana kodai iyayen yara ko kuma wakilansu.

Sai dai abin takaici a yau shine a Nijeriya ana jefa yara cikin kowanne irin nau’i na wahala, wanda hakan ka iya jawo givi ga ci gaban al’umma. Za a iya cewa muzgunawa yara wani abu ne da aka gado shi tun kaka da kakanni.Idan an lura za a ga irin yadda ake azabtar da yara a al’umomin mu , musamman ma a qauyuka, wai hakan yana daga cikin hanyar su ta ba wa yara ilmi da kuma tarbiyyantar da su. Shekaru aru-aru da suka wuce, halin da yara ke ciki na qara damun jama’a.

Cin mutuncin yara ko azabtar da su, abu ne da ya zama ruwan dare a Nijeriya saboda yardar mutane da cewa yara ba su da wani haqqi. Saboda haka matuqar ana so a tarbiyyantar da su to sai an dake su/ ko a hana su buqatunsu domin su gyaru. Wannan na aukuwa ne saboda irin riqon sakainar kashi da iyaye da mariqa da ma al’uma gaba xaya ke yi wa yara, ko da ya ke tun a farkon wannan qarni qasashen duniya suka maida hankalinsu wajen nemawa yara haqqinsu, amma duk da haka har yanzu yara na fuskantar cin mutunci.

Ana tilastawa yara shiga aikin neman kuxi, wanda hakan kan sanya yara xaukar talla suna yawo akan tituna, wasu kuwa a bada su a matsayin boyi-boyi (yaron gida) ga masu kuxi don kwaxayin baiwa yaran ilimi ko kuxi ga iyayen yaran, wasu yaran kan yi karen mota (kwandasta), wasu kuwa a xauke su ai’kin kafinta, walda, facin taya da kuma aikin kanikanci. Ana tilasta masu, su yi aiki har zuwa aqalla sa’o’ i goma a rana akan kuxin daba su taka kara sun karya ba, wasu yaran kuwa ana tilasta musu yin auren wuri wanda hakan kan sanya su yin jima’i tun suna qanana. A irin wannan yanayi yara za su iya fuskantar haxarin sacewa ko musayarsu da dukiya daga iyaye ko mariqa yaro.

Cin mutuncin yara ya zama ruwan dare a qasashe masu tasowa, cikinsu har da Nijeriya, ya kuma yiwo qasa zuwa cikinmu. A irin wannan tsari waxanda aka fi azabtarwar su ne mata.

Al’uma ta xauka yara ba su da haqqoqi, saboda su qanana ne. Har ila yau wai kuma kar yara mata su samu haqqoqi iri guda da yara maza, kuma al’umma kan yi fushi idan yara sun yi magana a game da haqqoqin su.

## TARON QASASHEN DUNIYA AKAN HAQQIN QANANAN YARA

**WANE NE YARO?**

Yaro shine duk wani mutumin da ke qasa da shekaru goma sha takwas.

**MENE NE HAQQI**

Wata baiwa da Allah ya yi wa mutum

Wata xabi’a ta shi.

Abubuwan da shari’a ta tanada.

Babban taron da majalisar xinkin duniya ta gudanar a ranar ashirin ga watan Nuwamba 1989 ya amince da yarjejeniyar majalisar akan haqqoqin yara. Domin kyautata rayuwar yara a ko'ina cikin faxin duniya, da kyautata martabarsu, da kare haqqoqinsu, har ila yau, da buqatar al'umma baki xaya ta mai da hankali akan abubuwan da su ka shafi lafiya da walwala da kuma dukkan wani abin da zai taimaka wajen ci gaban yara, Qungiyar UNICEP ta shirya wani taro na Yara ranar 29-30 ga watan satumba, 1990 a babbar ofishin majalisar xinkin duniya da ke birnin New york.

Shugabanni da gwamnatocin qasashe saba'in da xaya ne ciki har da Nijeriya suka halarci wannan taro tare da sanya hannun qulla wata yarjejeniya da kuma shirye-shiryen irin abubuwan da su ka kamata ayi waxanda za su tava rayuwar yara kaxai.

Taron na duniya ya yi sanadiyyar kafuwar taron majalisar xinkin duniya akan haqqoqin yara. A halin yanzu fiye da qasashe 198, ciki har da Nijeriya suka sanya hannu akan yarjejeniyar. Bayanai sun nuna ita ce yarjejeniya mafi karvuwa da ta game duniya. Kuma domin bin abubuwan da taron ya tanadar, qungiyar haxa kan Afirka (OAU) a taronta na shugabannin qasashe a Addis Ababa a 1990 ta amince da wata yarjejeniya akan haqqoqin yara da kuma kyautata jin daxin yaran Afirka.

Wannan yarjejeniya ta OAU da aka samo ta daga taron majalisar xinkin duniya, ta yi la'akari da yanayin zamantakewa da al'adunmu waxanda suka shafi yaran Afirka. Saboda haka yayin da taron majalisar xinkin duniya ke duba haqqoqin yara a duniya gaba xaya, ita yarjejeniyar OAU ta duba haqqoqin yaran da ke Afirka. Har wa yau domin jawo hankalin jama'a, daga bisani OAU ta faxi a Abuja 1991, cewa shekarun 1990, "qarnin yaran Afirka" kuma ta keve ranar 16 ga watan yuni na kowacce shekara ta zama "Ranar Yaran Afirka."

## <u>HAQQIN KOWANNE YARO</u>

1) Kowanne yaro yana da haqqin ya rayu kuma a qyale shi ya girma ya kuma bunqasa.
2) Kowane yaro yana da haqqin a raxa masa suna, sannan ya kasance yana da 'yanuwa kuma xan qasa
3) Ko wanne yaro ya na da 'yancin shiga dukkan wata qungiya ko taro kamar yadda doka ta yarje masa.
4) Ko wanne yaro yana da haqqin faxin ra'ayoyin sa da ikon isar da ra'ayayoyin na sa akan dukkan wani batu muddin doka ba ta yi hani akan hakan ba.
5) Kowanne yaro yana da haqqin a kare shi daga duk wani tsari da zai yin shisshigi cikin sirrinsa, ko martabar sa da mutuncin sa.

6) Kowanne yaro yana da ‘yancin samun isassehen hutu, walawa (nishaxi da wasanni) daidai shekarun sa da tsarin al’adunsa.

7) Kowanne yaro (namiji/mace) yana da ‘yancin soma karatun da ya wajaba, da kuma samun dama iri guda ta samun ilimi mai zurfi daidai gwargwadon qwazon kowane yaro.

8) Kowanne yaro yana da ‘yancin a kula da lafiyar sa kamar yadda ya kamata, da kare shi daga cututtuka, da kuma magance masa wata cuta da ta same shi domin ya rayu, ya girma ya kuma bunqasa.

9) Dole ne a kare kowane yaro daga qasqantarwa ko tursasawa musamman ta hanyar jima’I da miyagun qwayoyi, ci da qarfin yaro, azabtarwa, tozartarwa da kuma watsi da yaro.

10) Kada a nuna wa yaro wariyar launin fata ko qabilanci ko yare ko bambancin addini ko matsayi da dai sauran bambance-bambancen yanayin zamantakewar rayuwa.

**<u>HAQQOQIN DA SUKA RATAYA A WUYAN KOWANNE YARO</u>**

1) Haqqi da ya rataya a wuyan kowanne yaro ta fuskar taimakon iyayen sa da kuma al’ummar da ya ke cikin ta, da kuma garuruwan da ke Nijeriya da kuma sauran al’ummomin da doka ta amince da su a cikin qasa da kuma qasashen waje.

2) Baya ga shekaru da gwargwadon qarfin da yaro zai iya yin wani abu, akwai wasu haqqoqi da suka rataya a wuyansa kamar haka;

   a) Yin aiki domin cigaban iyalin da yake ciki,

   b) Mutunta iyayen sa, yayyensa da kuma na gaba da shi, sannan kuma ya taimaka musu idan buqatar yin hakan ta taso.

   c) Bautawa Nijeriya, ta yin amfani da jikin sa, da kuma samun qaqqarfar zuciya ta tunani da sanin ya kamata da kuma samun qwazo da ilimin da zai yi aiki da shi.

   d) Bayar da gudumawa ga abin da ya dace ga al’uma

   e) Karewa da kuma kyautata yanayin zamantakewa ta fuskar qarfafa haxin kan qasa saboda a cimma manufa daya.

   f) Karewa da kuma samun ‘yanci mai qwarin gaske tare da kare mutuncin qasa.

   g) Mutunta martabar ‘yanci, gaskiya da mutuntaka da adalci ga ko wane mutum.

   h) Kare martabar al’adun Nijeriya, da Afirka da qarfafa alaqa da sauran al’umma cikin aminci da haxin kai.

***3)*** Iyaye, da masu kula da yara, da cibiyoyi, da mutane da hukumomi, haqqoqi sun rataya a wayansu na kula, da biyan buqata, da tarbiyya, da ilimi, da horarwa, da xaukar aiki da kuma kyakkyawar kula da yaron da ke qarqashin kulawarsu kamar yadda aka tanadar masu damar neman ilimi, morewa ko fahimtar haqqoqin da aka zayyana a wannan vangare.

# HAQQOQIN DAN ADAM A MUSULUNCI

## ‘YANCIN YIN MAGANA

Kowane xan’adam yana da haqqin faxin albarkacin bakinsa a ko ta wacce hanya, ko dai ta mgana da baki ko a rubuce ko kuma ta kafofin yaxa labarai. Muna da kyakkyawan misali daga, Amirul Mumeenina Umar Ibn Khaddab, inda wani xan qasa ya qalubalance shi akan inda (Umar) ya samo mayafin sa. Sai Amiril-muminina ya yi wa al’umma cikakken bayani. (Hadisi).

## HAQQIN SAMUN ILIMI

“Nemi ilimi ko da a birnin sin ne domin kuwa ilimi wajibi ne ga kowane musulmi, namiji da mace. Qur’ani 96:1-5.

## HAQQIN TSAFTACE MUHALLI

“Tsafta rabin imani ce” Hadisi.

Abu Huraira ya ruwaito cewa Annabi yace “Ku Kaucewa abubuwa guda biyu na tsinuwa” sai aka tambaye shi waxanne abubuwa ne? sai ya bada amsa “mutum ya yi najasa a tsakiyar hanya da jama’a ke bi, ko kuma a inuwa inda jama’a ke zama” Hadisi.

## ‘YANCIN YIN ADDINI’

“Babu tilas a addini: gaskiya ta fita daban daga qarya .. Qur’ani 2:256 da 51:156s

## HAQQIN SIRRI:

‘Ya ku wadanda kuka yi imani! Ku kaucewa zargi domin kuwa zargi a wasu lokutan zunubi ne: kuma kar ku dinga leqen sirrin juna, ballantana faxin illa ga juna sa’ilin da waninku ya juya baya. Qur’ani 49:12 da 24:27-28.

## ‘YANCIN FADIN ALBARKACIN BAKI

Babu wani misali da aka tava samu a tarihi inda jama’a suka fito fili suna sukar shugaba (gwamnati) kamar lokacin mulkin halifa Umar. Wani mutum ya fito cikin jama’a yana mai faxin albarkacin bakinsa aka so a hana shi sai Khalifa ya ce “A bar shi ya faxa, saboda yana da damar albarkacin bakinsa. Babu amfani ace mutane ba sa faxin albarkacin bakin su, sannan kuma idan mu (masu mulki) ba za mu saurare su ba, mun zama marasa amfani” (RA) –Hadisi.

## HAQQIN YIN ADALCI:

“Ya ku waxanda kuka yi imani! Ku tsaya tsayin daka akan adalci, a matsayin shaidu ga Allah, ko da kuwa kai ta shafa, ko iyayenka, ko xanka, ko kuwa ta shafi mai kuxi ko talaka; Domin Allah ne ke iya yin babbar kariya ga dukkansu. Kar ku bi son (zukatanku), kar ku mance ku yi adalci, domin kuwa lallai Allah na sane da dukkan abubuwan da kuka aikata” Quran 7:29.

**HAQQIN DAIDAITON JINSI:**

Ba zan vata aikin ma'aikaci a tsakaninku ba, namiji ne ko mace" Qur'an 3:195

**KARIYA DAGA AZABTARWA:**

Ibn Umar ya ruwaito cewa Annabi ya tsinewa wanda ya azabtar da rai (Bukhari da Muslim) har ila yau a duba Qur'an 24:33; 4:92 da 9:60

**HAQQIN MALLAKAR DUKIYA**

……Kuma saboda haka, dukkan waxanda ke son su nema, su nema …" (daga dukiya da kasuwanci) Qur'an 83:26 da 4:4 – 7.

**HAQQIN RAYUWA:**

Kar ku xauki rai, wanda Allah ya tsarkake shi, sai dai ta hanyar shari'a da doka. Saboda haka ya umarceku, domin ku iya koyon hikima. Qur'an 5:32-34 da 2:179.

**HAQQOQIN TSIRARU DA GAJIYAYYU**

Annabi (S.A.W) Yace "Na fada maku 'yan aljanna? Shine dukkan wanda ya ke gajiyayye wanda kuma aka xauke shi a matsayin gajiyayye, kuma ake yi ma shi kallon qasqanci, wanda in ya rantse da Allah zai cika ta …" Hadisi (Bukhari da Muslim v. 21).

**HAQQIN SHIGAR DA QARA**

Dokar Musulunci ta ba wa ko wane xan adam haqqin Shigar da qara, Mutum ya na da damar kai qarar gwamna ko alqali ko Khalifa idan har suka musguna masa. Babu shamaki ga waxanda aka zalunta. (ibn kadiri shahararren mahaddacin Al'kur'anin nan ya fadi shari'ar da aka yi tsakanin Ali Ibn Talib da kuma wani bayahude, da kuma yadda alqalin ya yi shari'ar) Hadisi.

**KARE MARAYU**

A kuma ba wa marayu dukiyarsu kuma kar a musanya masu abubuwan (ku) marasa kyau da (na su) ma su kyau; kuma kar ku kwashe mu su kayansu (ta qarawa) akan naku. Lallai, wannan babban zunubi ne. Al Nisa'a 2.

**HAQQIN SHAYARWA**

"Mata ke shayar da abinda suka Haifa … idan uba ya buqaci ya cika qa'idar. Amma shi zai' xau nauyin abinci da tufatarwa daidai-wa-daida… Babu uwa da za a nuna wa wani bambanci Saboda xanta, ko da uba …… Qur'an 2:233.

**HAQQIN YIN TAFIYA KO QAURA**

Wanda ya yi hijira (daga garinsu) saboda Allah, zai samu a doron qasa wuraren zama da dama domin rayuwa …. Nisa'a Qur'an 4:100.

**HAQQIN WANDA AKE BI BASHI**

Idan wanda ake bi bashi na cikin mawuyacin hali, a qara ma sa lokaci, har sai al'amura sun yi sauqi gare shi. Qur'an 2 :282

**YANCIN YIN AURE**

"Kuma daga alamomin  shine wannan, cewa ya qirqiro maku mataye daga gareku, domin samun hutu a gunsu, kuma ya sanya a tsakaninku qauna da rahama a tsakaninku, lallai, a nan alamu ne ga mutane da su ka yi tunani. Qur'an 30:21 da 4:3

**HAQQIN YAFEWA : (GA WAXANDA SUKA TUBA)**

« idan xaya daga cikun ku ya aikata laifi a cikin rashin sani amma kuma daga baya ya tuba ya gyara, Lalle Allah  mai rahama ne mai jin qai » kur'an 6 :54

**HAQQIN NEMAN ABINCI**

Zubair Ibn Awam ya ruwaito cewa Annabi ya ce "Dayanku ya xauki Igiyarsa, ya je tsauni, ya yo ice a bayanshi, ya je ya sayar ya fita kunyar Allah, ya faye mashi da ya je ya na roqon jama'a, ko su bashi ko su hana shi, Hadisi na (bukhari) kuma a duba (Q62:11).

**HAQQIN TSARO**

Haqqin gwamnati ne ta samar da tsaro a inda al'umma ta taru da yawa (Al kifayah wal Ghima)

**HAQQIN QIN BIYAYYA GA AIKATA ZUNUBI**

"Babu biyayya ga dukkan wata halitta da ke qin biyayya ga mahalicci". Kuma; "ana biyayya ne ga abinda yake halal ne" Hadith da kuma Qur'an 31:15

**HAQQIN KYAUTATAWA MATA**

"Ku daxaxa musu cikin jin daxi" Qur'an 4:19

"Kar namiji musulmi ya kushe mace musulma, in bai so wani halinta ba, ya yi sha'awar wani" Hadisi.

**HAQQIN KULA DA MATA**

"Maza ne masu kare mata da kuma kula da su ……." Qur'an 4:34

**HAQQIN YIN SHUGABANCI NA GARI**

"… mayar da amana ga waxanda su ke da ita kuma in ka na shari'a tsakanin mutane… yi shari'ar da adalci…" Qur'an 4:59

**HAQQIN SAMUN LAFIYA**

Kar ka hana jikinka (lafiya) abinda ya cancanta. Hadisi  ne da aka amince dashi.

# KARIYAR DA DOKA TA TANADAR

## MANUFOFI

A qarshen wannan littafi masu karatun za su iya:

- *Gane ma'anar kariyar da doka ta yi*
- *Faxin tanade-tanaden da suka kare yara*
- *Yabawa dokokin da suka kare yara*
- *Sanin cikakkiyar ma'anar yarjejeniyar CEDAW*
- *LIssafa wasu daga cikin Haqqoqin da CEDAW ta tanadar.*

**GABATARWA:**

A qoqarin bayyana ma'anar kariyar da doka ta yi, za mu dubi kalmomi uku na ingilishi domin kara samun haske a game da ma'anar.

**LAW:** (**Doka**): waxannan wasu dokoki ne da hukuma ta tanada, da al'uma ta amince da su a matsayin doka

**LEGAL:** (**Shari'ah**): Wannan shine dukkan wani batu ko al'amari da yake da nasaba da doka ko ya yi daidai da dokar mulki.

**PROTECTION: (kariya)** Wannan shine kare Mutum ko hana dukkan wani abu da zai cutar da shi ko ya ji ma sa rauni.

Saboda haka kariyar doka na nufin yin amfani da dokar Mulki ta qasa da ake da ita, domin kare wani Mutum, ko wani wuri ko kuma wani abu. Wannan xan littafi na magana ne akan kariyar da doka ta yi da kuma amincewa da haqqoqin yara da mata a cikin dokokin.

Jawabi na farko cikin Jawabai talatin da xaya (31) da ke cikin jawaban majalisar xinkin duniya akan yara, ya bayyana yaro a matsayin " dukkan wani xan adam da bai haura shekaru goma sha takwas ba'. Ma'anar za ta iya bambanta saboda bambance-bambancen da ake da su a tsakanin dokokin garuruwa, za a iya samu ya gaza wannan ma'anar da Majalisar xinkin duniya ta bayar. An kuma yi tanadin cewa kowane yaro yana da haqqin ya rayu. Wannan haqqi na rayuwa yana nufin dukkan sauran haqqoqi da ake ba wa xan adam baligi ko tsoho.

<u>**ABUBUWAN DA SUKA CANCANTA A BAIWA KOWANE YARO**</u>

**IYALI:**

Wannan shine abin da ya fi komai kusa da yaro, Iyali na ba da muhimmiyar gudunmawa ga rayuwar wanda ya ke cikin sa. Yana ba da rayuwa ga sabon jaririn da a ka haifa, da shayarwa, da tufatar da shi, da makwanci, da ilimi da kuma kare shi daga wani haxari ga rayuwarsa, da kuma nuna masa qauna ba ta son zuciya ba a ko wane lokaci. Wannan ya shafi baiwa yaro tarbiyya ta farko daga haihuwarsa. Dukkan wani abin da zai iya kawo matsala ga zaman lafiyan iyali, to lallai zai iya kawo cikas ga rayuwar yaro. Iyaye da kuma mariqan yaro ne ke da haqqin taso da yaro cikin managarciyar rayuwa.

Ga ‘ya mace kuwa iyalan ta ne farin cikin ta, saboda haka yarinya qarama na buqatar so na musamman da kuma kula daga iyayenta da ‘yan uwanta: A Ciyar da ita a kuma ba ta ilimi daidai da kowa, sannan uwa uba yancin faxin albarkacin bakinta da kuma ra’ayinta. Yarinyar da ta balaga na da ‘yancin zavar abinda take so a tafiyar da sha’anin gidansu (Iyali), kula da yara da ilimi da kuma dokokin da ke tafiyar da gidansu.

**DOKA:**

Gwamnati ta kare yara a qarqashin doka mai taken “Dokar yara da matasa”. Wannan doka ta yi tanadin hanyoyin kula da kuma yadda za a yi da yaron da ya karya doka;

1. Bayar da beli
2. Gwamnati ta ajiye yaro a hannun ta idan ba ayi belin sa ba.
3. Yin iyaka akan ikon da kotu ke da shi na ladabtar da yaron da ya karya doka.
4. Iyaye ko mariqan mai laifi ne za su halarci kotu.
5. Samar da jami’an bada shawarwari ga yaran da suka karya doka.

## <u>Doka ta bayyana cewa laifine a:</u>

1. Yi musaya ko a sayar da kangararren yaro.
2. Bayar da riqon kangararren yaro a hannun wani in ba xan uwa na jika ba.
3. Sanya yaro cikin haxarin aukawa munanan halaye kamar karuwanci ko bauta ko cikin qangi ko kuma bara.
4. Ci da gumin yaro, wato amfani da qarfin sa fiye da qima domin samun kuxi

5. Azabatarwar, ko tursasawa, ko watsi da yaro ta yadda zai yi sanadiyyar yaro ya wahala ko ya faxa wani hali da zai shafi lafiyarsa kamar makancewa, ko kurumcewa, ko nakasa ta jiki ko gurgunta, ko tavin hankali.
6. Amfani da yaro wajen yin bara, ko kasuwanci ko talla.

**KOTU:**

Gwamnati ta yi dokoki da suka shafi yadda za a tafiyar da shari'ar laifuffukan kangararrun yara. Idan aka gudanar da kotunan kamar yadda ya kamata za su zamanto misali ne ga cewar dokar na aikin ne ta nazarin halayyar xan adam da kuma nazarin zamantakewa.
A Nijeriya, ana tafiyar da kotunan ne kamar yadda dokar yara ta tanadar, ko da ya ke babu takaimamman iyaka tsakanin manyan laifuffuka qanana.

**YAN SANDA:**

Waxannan su ma wata hanya ce da ake amfani da ita wajen kare yara. Ita wannan hanya ba wai kawai ta na da qarfin kama kangararrun yara ba ne, har ma da manya waxanda suka karya dokar da ta shafi haqqoqin yara. Ya bayyana cewa a Najeriya babu wani cikakken wayar da kai ko tsarin ladabtar da manyan da suka karya dokar ta shafi haqqoqin qananan yara saboda wasu dalilai da za mu gani nan gaba. Saboda haka, aikin 'yansanda ne su tabbatar da cewa ba a haxa yaron da aka zalunta da waxanda ke da laifuka ba, sannan kuma a tabbatar da cewa an kula sosai da mai laifin da ke qarqashin kulawar 'yansanda wajen samun cikakken tsaro da kulawa.

**KULAWA DA JIN DAXIN ZAMANTAKEWA:**

Wannan shima wata hanya ce da gwammanti ke amfani da ita wajen kare yara. Jami'in kula da jin daxi na taimakawa jama'a musamman wajen yadda za su taimaki kansu. Taimakon da jami'an kula da jin daxin kan bayar sun haxa da maza da mata, da iyaye maza da mata da yara da ke matakin ko wane shekaru. Hakanan yaran da iyayensu suka rabu kuma ba a lura da su kamar yadda ya kamata, suna samun taimako daga ofishin, musamman wajen mayar wa da iyaye nauyin da ya rataya a wuyansu. Har wa yau jami'an jin daxin na kuma aiki da haxin guiwar kotunan kula da laifukan kangararrun yara domin bada shawarwari da kuma nutsar da kangararrun yara.
Ta fuskar 'yan mata ko matan da a gida ko cikin iyali aka ci zarafinsu ta kowace hanya ce, za su iya zuwa ofishin jami'an kula domin neman taimako. Mata da aka bari da wahalhalun yara su kaxai ko kuma ke wahala wajen samun kuxin kulawa da yara daga mazajensu da suka rabu da su, sai su nemi taimako a wajen ofishin jami 'an mafi kusa.

**HUKUMAR KULA DA LAFIYA:**

Ma'aikatar lafiya ce ke da nauyin samar da wadatattun kayan kula da lafiyar yara. A Nijeriya har yanzu akwai buqatar a samar da qarin kayayyakin kula da lafiya ga yara qanana tare da buqatar qarin likitocin yara.

# HAQQOQIN MATA

Haqqin mata a nan na nufin kwatantace da na maza a kowace al'umma. Al'umma a da ta na rarraba matsayi da nauye-nauye, da abubuwan yi, da waxanda ba a so ga mata. A kowane lokaci wannan abu ana tsara shi ne ba tare da tuntuvar ra'ayin matan ba, ko ma ba tare da saninsu ba. Wannan vangare na wannan littafi ba wai ya na son ya sanya mata su fifita akan maza ba ne, illa dai kawai duba da idon basira a gani mene ne mafi adalci da kuma dacewa. Zamu duba yarjejeniyar CEDAW sa'ilin da muke qoqarin tuna cewa "kowa yaci ladan kuturu to dole ne yayi masa aski"

**CEDAW:** (Convention On The Elimination Of All Forms Of Discrimination Against-Women), Wato taron soke dukkan wani nau'i na nunawa mata wariya. Yarjejeniyar ta tanadar da daraja ko matsayi iri guda tsakanin mata da maza. Babban taron majalisar xinkin duniya ya amince da waccar yajejeniya a ranar 18 ga watan Disambar shekarar 1979, ta kuma soma aiki a ranar 3 ga watan Satumba shekarar 1981. A watan Disambar shekarar 1993, qasashe 130 ne suka sanya hannu cikin wannan yarjejeniyar. Yarjejeniyar na da wani kwamiti mai qunshe da qwararru 23 masu zaman kansu waxanda sune za su yi nazarin rahotannin da qasashen da suka amince da yarjejeniya, kuma suka sanya hannu a kanta suka gabatar akan matsayin mata.

Taron na soke dukkan wani nau' I na wariya ga mata, ya bayyana ma'anar wariya ga mata da cewa ta haxa da: dukkan wani bambanci, hani, ko kevewa da aka yi masu saboda jinsi, wanda zai iya hana su morar haqqoqkin da suka shafi siyasa da tattalin arziki da zamantakewa, da al'adu, da sauran su. Yankunan kundin yarjejeniyar da dama sun tavo batutuwa kamar haka.

1. Yanki na biyu na taron ya buqaci gwamnati ta soke bambanci da ake nunawa mata da kuma wajabta akan gwamnati ta xaukaka daidaito da tabbatar da cikakken cigaba da kuma havakar mata ta hanyoyin da tsarin mulki ya amince da su, da shari'a da kuma sauran hanyoyin da suka dace.
2. Dokoki da matakai: - Yankin ya buqaci dukkan qasashe da su xau matakan da suka dace domin baiwa mata tabbacin walawa da kuma morar 'yanci akan tafarkin daidaito da maza a dukkan fannoni musamman a fannin siyasa, da zamantakewa da tattalin arziki da al'ada.
3. Matakan wucin gadi: matakai na hanzarta daidaito tsakanin maza da mata na cewa "Ana buqatar qasashe su xau matakan wucin gadi domin hanzarta tabbatar da daidaito tsakanin maza da mata"

4. Jinsintawa tare da yin gyara ga al'ada. Yankin ya buqaci qasashen da ke cikin yarjejeniyar su xau dukkan matakan da suka dace domin;
   a. Canja tsarin zamantakewa da al'ada ke amfani da shi a tsakanin maza da mata domin cimma manufar soke bambanci, da dukkan sauran dabi'u da suke da salsala da batun nuna qasqanci da fifiko a tsakanin kowanne xaya daga cikin jinsin, ko ta tsarin rawar da ake bambancewa maza da mata su taka;

   b. Tabbatar da ilimin iyali ya haxa da fahimtar muhimmanci da gudunmuwar mata a cikin al'umma da kuma fahimtar amfaninsu wajen tarbiyyantar da yaransu, musamman idan aka yi la'akari da cewa tarbiyyantar da yara abu ne mai matuqar muhimmanci ta kowacce fuska.
5. Fataucin mata da karuwancin su: wannan yanki a taqaice ya na gayyatar dukkan qasashe da su xau matakan da suka dace domin rushe karuwanci da dukkan wani nau'I na ci-da ceto ta fuskar jima'i da fataucin mata.
6. Siyasa da rayuwa ta yau da kullum, Wannan yanki ya buqaci qasashen da ke cikin wannan yarjejeniya su xau mtakan da suka dace domin kawar da wariyar da ake nunawa mata a fuskar siyasa da rayuwar yau da kullum ta kasa da kuma tabbatar da daidato, a haqqoqin:
   a. Yin zave a dukkan zavuvvuka,
   b. Shiga a dama da su wajen gudanar da tsare –tsaren gwamnati
   c. Shiga qungiyoyin da ba na gwamnati ba da suka damu da rayuwar jama'ar qasa.
7. Mata a fagen siyasar duniya: Wannan yankin ya buqaci qasashe "su baiwa mata damar wakiltar gwamnatin su a duniya da kuma shiga cikin ayyukan qungiyoyin qasashen duniya.
8. Haqqin zama xan qasa: Wannan yanki ya nemi qasashen da ke cikin yarjejeniyar su baiwa mata iko iri guda da na maza, wajen samar da, ko canzawa ko ci-gaba da riqe shaidar qasar da take ciki. Ya kamata qasashen su tabbatar auren baqon haure, bai shafi yancin matar ta fuskar qasarta ba. Yankin ya ci gaba da buqatar cewa qasashen su baiwa mata haqqoqi iri guda da maza ta fuskar qasar da 'ya'ya za su kasance.
9. Daidaito a haqqoqin ilimi; wannan yanki ya gayyaci qasashe su xau dukkan matakan da suka dace domin kawar da wariya a mata da samara da daidaito tsakaninsu da maza ta fuskar ilimi. Musamman anan yanki na (10) ya yi qira a madadin yara maza da mata:
   a. Samar da daidaito wajen koyan aiki da sanao'I da samara da nagartaccen ilimi sannan da dama iri guda wajen mallakar shaidar karatu.

b. Dama iri guda ta samun tsari na cigaba da neman ilmi, ciki har da shirin yaqi da jahilci mai tasiri, kuma mai manufar rage givin da kan auku tun farko ta fuskar ilmin maza da mata.

10. Xaukar aiki da Qwadago: Wannan yanki ya buqaci qasashen su xau matakan da suka dace domin kawar da bambancin da ake nunawa mata a vangaren xaukar aiki domin tabbatar da samar da daidaito tsakanin maza da mata, musamman akan.

a. Haqqi iri guda na xaukar aiki, da ya haxa da amfani da tsari iri guda na zaven waxanda za a xauka aiki.

b. ‘Yancin zavar sana’a, aiki, horaswa, koyon sana’a da zurfafa koyon sana’o’in hannu.

c. Lada da haqqoqi iri guda, da suka haxa da tsarin aiki iri guda, daraja iri guda, da daidaito na ma’aunin darajar aikin.

d. Haqqoqin samun tsaron rayuwa, musamman bayan an yi ritaya, ko matsalar rashin aiki, ko rashin lafiya, ko nakasa ko tsufa ko dai sauran gazawa ta aiki da haqqin samun kuxin hutu.

e. Kula da lafiya da kare mutum a wajen aiki

f. Samar da takunkumin da zai hana kora daga aiki saboda samun juna biyu ko wasu xabi’u. Sannan a vullo da ba da hutun haihuwa tare da kuxin hutu.

g. Ba da qwarin guiwar samar da abubuwa na kyautata jin daxi, da suka hada da kula da yaro.

h. Kariya ta musamman ta hana yin aiki haxari yayin da ake da juna biyu.

Yankin ya buqaci qasashe waxanda ke cikin yarjejeniyar su samar da dokoki na kariya da suka shafi batutuwan da wannan yanki ya yi magana akai, da kuma sake nazarin waxannan dokoki lokaci lokaci ta la’akari da canje canjen da ake samu ta fuskar ilmin kimiyya da fasaha da kuma sabunta dokokin, ko a yi sauyi ko a yi qari a inda ya kamata.

11. Kula da lafiya da tsarin iyali. Wannan yankin ya buqaci qasashen da ke cikin yarjejeniyar su xau dukkan matakan da suka dace domin kawar da bambanci da ake nunawa mata a vangaren kula da lafiya, da tsarin iyali, qasashen su tabbatar sun yi wa mata masu juna biyu aikace aikacen da suka kamata, kafin da kuma bayan sun haihu. Samar masu da abubuwan kula da lafiya kyauta a inda buqatar hakan ta taso, da kuma isasshen abinci mai gina jiki sa’ilin juna biyu da lokacin shayarwa.

12. Samar da rance ko basussuka, da morar abubuwa na tattalin arziki da zamantakewa. Ana buqatar qasahe su xau matakan da suka dace domin kawar da bambanci da ake nunawa mata a sauran vangarorin tattalin arziki da rayuwa ta yau a waxannan vangarori;

a. Haqqin amfana da abubuwan da iyali ya kamata su mora;

b. ‘Yancin samun rance/bashi, na banki da rance na mallakar gini da sauran ire-iren rance na kuxi.
c. Haqqin shiga abubuwa na motsa jiki, da wasannin da dukkan bangarori na al’adu.

13. Mata a aikin gona – Matan karkara: Ana so qasashe su yi la’akari da wasu matsaloli da matan karkara ke fuskanta da kuma muhimmiyar rawar da matan karkarar ke takawa a cigaban tattalin arziki da rayuwar iyalansu, da ayyukansu a vangarorin da ba a basu muhimmaci ta fuskar tattalin arziqi, kuma za su xauki dukkan matakan da suka dace na aiwatar da wannan yarjejeniya ga matan da ke yankunan karkara; qasashen da ke cikin yarjejeniyar za su xau matakan kawar da bambanci da ake nunawa mata a yankunan karkara kuma za su kasance a cikin duk wani tsari sannan da kuma amfana da haqqoqin;
a. Kasancewa cikin shirin faxaxawa da kuma aiwatar da tsare-tsaren cigaba a kowanne mataki,
b. Samun isasshiyar kula da lafiya ta fuskar tsarin iyali
c. Amfana daga tsaro na zamantakewa
d. Samun dukkan ire-iren horaswa da ilmi kowanne, da qwaqqwaran iya karatu da rubutu.
14. Daidaito a gaban doka: wannan yanki ya buqaci qasashen da ke cikin yarjejeniyar su tabbatar da daidaito tsakanin maza da mata a gaban doka a al’amura da suka shafi jama’a da haqqoqi na shari’a. Yankin ya yi kira ga qasashe su soke dukkan abubuwa masu zaman kansu, waxanda suka taqaita haqqin mata. Yankin ya cigaba da yin kira ga qasashen da su baiwa maza da mata haqqi iri guda na zavar jurewarsu da kuma mazauni.
15. Aure da al’amura na zaman aure: Wannan yankin ya nemi a xauki dukkan matakan da suka dace na kawar da wariya da ake nunawa mata a dukkan al’amuran da suka jivanci aure, da dangantakar iyali da kuma tabbatar da dasa tubalin daidaito tsakanin maza da mata.
a. Haqqi iri guda na shiga aure
b. Haqqi iri guda na ‘yancin zavar abokin zaman aure da kuma yin auren cikin yardar su da kuma cikakkiyar masaniyar su.
c. Haqqoqi da nauye-nauye iri guda yayin auren da kuma lokacin kashe auren.
d. Haqqoqi da nauye-nauye iri guda a matsayinsu na iyaye, ko da kuwa wane matsayi ne na aure mutum yake, a al’amura da suka jibanci ‘ya’yayensu kuma, kare buqatar yaran ya zama muhimmi.
e. Haqqoqi iri guda na ‘yancin yanke shawara, akan yawan yara da za su iya xaukar nauyi dakuma irin tazarar da za su bayar tsakanin yaransu da kuma dammar samun isassun bayanai, da ilmi da kuma damar aiki da waxannan haqqoqi

f. Haqqoqi da nauye- nauye iri guda ta fuskar kulawa, da riqon amanar yaro, da goyo, ko cibiyoyi makamantan waxannansu da ake aiwatar da irin waxannan abubuwa kuma suna nan qunshe cikin dokokin qasa, domin kare buqatun yara, wanda shine muhimmi a kowanne.
g. Haqqi iri guda na qashin kai, a matsayinsu na mata da miji, da ya haxa da haqqin zavar sunan da za a kira iyalin da shi, ko wata sana'a da aiki
h. Haqqi iri guda ga ma'auratan biyu ta fuskar mallaka, ko samu, ko tafiyarwa ko kuma sayar da abin da aka mallaka.
i. Baiko da aure na yaro ba shi da wata hujja ta shari'a, kuma za'a xauki dukkan matakin da ya dace domin fayyace mafi qarancin shekaru na yin aure, da kuma miqa buqatar yin aure a dukkan wuraren yin rajista wajabtattu na hukuma
j. Yarjejeniyar qasashen duniya akan 'yancin xan'adam (yanki na biyu) na cewa kowanne mutum yana da 'yancin dukkan haqqoqi da 'yancin da aka tsara a cikin wannan yarjejeniya ba tare da nuna bambanci ta fuskar launin fata, al'uma, ra'ayi, qasa, usuli na zamantakewa, dukiya, haihuwa ko dai sauran wani matsayi ba.

**KETA HAQQOQIN MATA**

- Bada fifiko ga xa namiji
- A al'uma, ana rarraba nauye-nauye da suka savawa juna ga yara maza da yara mata, da bambancin zavar aiki ko abinda suke so su zama nan gaba, da shekaru daban-daban na aure.
- Tsarin a dake ka a hana ka kuka, ma'ana (maza ne kaxai za su fi samun biyan buqata yayin jima'i)
- Tsananta zancen budurci ga yara matakawai ban da yara maza.
- Yi wa mata kaciya da sauran dabi'u da ke da illa ga mata
- Taqaita shugabanci ga yara maza kawai.
- 'Yan mata su yi girki, da talla, da ayyuka na cikin gida da kuma kula da yara.
- Mata kan sadaukar da rayuwar su, musamman wajen haihuwa amma duk da haka ba a basu damar bayar da shawara akan wasu al'amura.
- Maza ne ke da yancin riqe yara idan aure ya mutu.
  a kowanne lokaci
- Mata basu da ikon gado
- Bambanci wajen rarraba ayyukan gida, a yau akwai mata da dama da suka yi fice wajen riqe muqamai masu muhimmanci, amma duk da haka sai ta yi ayyukan gida.

MANAZARTA

1. Human Rights in Nigeria Bankole Olubamise – 1998

2. Law Relating to Children in Nigeria by: UNICEF 1988